# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na goma: Hangen Dala ba shiga birni ba ne

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya tace: Ludger Schadomsky da Maja Braun
Wanda ya fassara: Yusuf Idris

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| Mai hayan 'yan wasa: | ɗan shekara 40 |
| Mr. Madu: | ɗan shekara 54 |
| 'Yar jarida: | 'yar shekara 25 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |

**MAI GABATARWA:**

Jama'a, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin shiri na goma kuma na ƙarshe a kan harkar wasan ƙwallon ƙafa a Afirka**.** A cikin shirin da ya gabata, kun ji yadda wasan sa da zumunci tsakanin ƙungiyar wasan ƙwallon ƙafa ta garin Gabas da 'yan wasan nan na ƙungiyar Metogba ya watse bayan wasu 'yan tsiraru sun ta da rigima a filin wasan, saboda Zakari ya jefa ƙwallo a ragar ƙungiyar da suke goya wa baya. Dangantaka tsakanin Honourable Gambo da ɗanshi ta yi ƙamari, saboda sa hannu da ya yi har 'yan sanda suka kama Zakari. A ɓangare ɗaya kuma Shehu, babban abokin Zakari a da, ya nuna halinshi na gaskiya bayan Zakari ya kai mishi ziyara a caji-ofis. Sannan Anti Lily ta ƙi yi wa Honourable Gambo bayani a kan wani abu da ya faru tun da daɗewa. Yanzu kuma me zai biyo baya? A kasance da mu a cikin shirin na yau, inda za mu faro daga ɗakin canza kaya na 'yan wasa.

**Fitowa ta 1: A ɗakin canza kaya na 'yan wasa**

Zakari, Safina, John, Metogba, Mai hayan 'yan wasa

**METOGBA:** Zan ba ku haƙuri saboda an tsai da wasan. Ba laifinku ba ne. Saboda kun ci ƙwallo ne ya sa kurum wasu marasa hankali suka ta da rigima. Ina alfahari da ku sosai. Saboda haka, yanzu lokaci ya yi da zan faɗi ɗan wasan da ya yi fice...

**MAI GABATARWA**:

A yayin da Metogba ke shirin faɗin ko wane ne ɗan wasan da ya yi fice a wasan da aka yi, Honourable Gambo ya yi ƙokari har ya kai ga inda Ant Lily take kuma, tare da taimakon mai tsaronshi, sun fitar da ita daga cikin filin wasan ba tare da wata matsala ba zuwa wurin da ya ajiye motarsa. A can ɗakin da 'yan wasa ke canza kayan kuma...

**METOGBA:** Saboda haka za ku yarda da ni cewa, ɗan wasan da ya yi fice ...

**MAI HAYA:** Sannunku dai! Ni mai farautan 'yan wasan ƙwallon ƙafa ne, kuma bari in fara da jinjina muku saboda irin wasa ya burge jama'a. Abin haushi, ba a bari an gama wasan ba. Ba zan ɓata muku lokaci ba. Na san cewa kun san abin da ya kawo ni nan. Wannan takardar kwanturagi ce ga yaron da ya ci ƙwallon da aka ci a wasan. Zai yi kyau in da za ka sa hannu yanzu. Haka zai ba ni damar fara yin duk wasu shirye-shirye da zai sa ka zo Turai ka fara wasa.

**METOGBA:** Yallaɓai, ina ganin ka ɗan makara. Ɗan wasan da kake so ka ɗauka, shi ne ɗan wasan da nake so in sanar da cewa, shi ne wanda ya yi fice a wasan. Wannan ɗan wasan kuwa shi ne Zakari. Saboda haka, Zaks, in kana so kana iya shiga ƙaramar ƙungiyarmu ka fara wasa, har sai ka cika shekaru goma sha takwas.

**SAFINA:** Ina taya ka murna, Zaks! Buƙatarka ta biya! Wallahi, al'amarin sai hamdala.

**MAI HAYA:** Ina ganin ai da mun ƙyale shi ya yanke wa kanshi shawara ko? Zakari me kake so? Ka yi wasa a ƙaramar ƙungiyar ko kwanturagina?!

**ZAKARI:** Ni ban sani ba. Abubuwa sun zo min a gaba ɗaya, kuma a lokaci ɗaya. Ina buƙatar lokaci.

**MAI HAYA:** Ni kuma ba ni da lokaci. Yau da daddare jirgina zai tashi, kuma ina buƙatar in tafi da kwanturagin da aka sa hannu a kanshi. Saboda haka in ba kai ba, wataƙila wanda ya yi bugun kusarwar? Yi haƙuri, ban san sunanka ba. Kai! E, kai ɗin!

**JOHN:** Ni? John. Sunana John. E! Zan so in sa hannu a kwanturagin.

Zan sa hannun yanzu-yanzun nan!

**MAI HAYA:** Ya yi kyau! To, ga takardun. Kar ka damu kanka da karanta kome. An kammala kome yadda ya dace. Ka sa hannu kawai a ƙarshe, inda aka rubuta "ɗan wasa".

**METOGBA:** Yallaɓai, in ba ka damu ba, zan so in yi magana da 'yan wasa na mu kaɗai kawai.

**MAI HAYA:** Na kusa gama abin da zan yi. Zan karɓi takardun bayan John ya sa hannu, sai in wuce.

**METOGBA:** E, na sani. Amma dai ina buƙatar ka ba mu minti ɗaya kawai kafin John ya sa hannu ko ma mene ne.

**MAI HAYA:** To shi ke nan. Ina jira a waje.

**MAI GABATARWA**:
'Yan wasa da yawa sun sha faɗa wa hannun masu hayar 'yan wasa, da ke musu alƙawarin kwanturagi mai tsoka, wanda suke ganin zai sa su iya mallakar duk wani abu na duniya, amma daga baya, sai ta zama musu hanyar wahala mai tsanani. Wannan na ɗaya daga cikin irin waɗancan ne? Kuma yaya za a yi ɗan wasa ya kauce wa faɗa wa hannun irin waɗannan mutane? Za mu gane nan ba da daɗewa ba. Amma, bari mu koma wajen Honourable Gambo da Anti Lily, a yayin da suka shiga motarshi, kuma suna sauraron labari da ɗumi-ɗuminsa wanda ake watsawa kai tsaye a gidajen rediyo da talabijin.

**Fitowa ta 2: A babban filin wasa**
Mr. Madu, 'Yar jarida

**'YAR JARIDA:** Jama'a masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa a cikin wannan shirin. Kamar yadda muke kawo muku rahoto, kun ji cewa an dakatar da wani wasa tsakanin babbar ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta garin Gabas, da wata 'yar ƙaramar ƙungiya ta matasa tun kafin a je hutun rabin lokaci, bayan magoya bayan ƙungiyar ta garin Gabas sun fantsama cikin fili, bayan an jefa ƙwallo a ragar ƙungiyarsu. Shugaban ƙasa kanshi ya samu halartar kallon wasan. A tare da ni a ɗakin gabatar da shirye-shirye ina tare da shugaban ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa na garin Gabas, Mr.Madu, wanda zai yi mana fashin baƙi a kan yadda wasan ya gudana. Barka da warhaka Mr. Madu.

**MR. MADU:** Yauwa, barkanki dai.

**'YAR JARIDA:** To yanzu, wane mataki za ku ɗauka a kan waɗanda suka jawo sanadiyyar dakatar da wasan da aka yi?

**MR. MADU:** Yanzu bari in fara da gode wa Allah saboda ba wanda ya ji ciwo a cikin yamutsin da ya auku. Na biyu kuma, a matsayina na shugaban ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa a wannan ƙasa, na yi Allah wadai da wannan mummunan aiki. Kuma ƙungiyata za ta zauna ba da wani ɓata lokaci ba, don ta fito da sakamako mai zafi ga waɗanda suka jawo wannan ta'asa.

**'YAR JARIDA:** To, wannan na nufin cewa ita ma ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta garin Gabas za a hukunta ta ke nan?

**MR. MADU:** Ba zan ce kome ba dangane da wannan yanzu. Amma ina tabbatarwa da duk wani mai ƙaunar wasan ƙwallon ƙafa cewa za a yi bincike sosai a kan abin da ya faru, kuma duk wanda aka samu da laifi, to zai ɗanɗana kuɗarsa, ko da

kuwa shi wane ne.

**’YAR JARIDA:** Shin muna iya magana a kan ɗan yaron nan da ya ci wanda ya yi bugun kusurwar har ƙungiyarsa ta sami nasara a kan wasan?

**MAI GABATARWA:**
A yayin da aka ci gaba da tattaunawar, a can ɗakin canza kayan ’yan wasa kuwa...

**Fitowa ta 3: A ɗakin canza kayan ’yan wasa**
John, Metogba

**METOGBA:** John, kana hauka ne? Yaya za a yi ka sa hannu a kan kwanturagi ba tare da ka karanta abin da yake ƙunshe da shi ba? Kowa ya saurare ni! Na san cewa kowa yana da buƙatar ganin cewa ya zama ƙwararren ɗan wasa a Afirka. Amma ku san da cewa, ba kowace zuma take da zaƙi ba.

**JOHN:** To amma…amma fa…*Coach*, daga Turai fa ya zo. Ai ina ganin wannan ba wata matsala ba ce. A can ne fa dukkan ’yan wasan da suka yi fice suke wasanninsu.

**METOGBA:** Sai me? Kawai daga ya fito daga Turai sai ka yarda da shi? Bari in faɗa muku gaskiya. Ba dukkanku ba ne za su yi fice a harkar wasan ƙwallon ƙafa. Amma kar ku yarda wani ya yi amfani da rashin saninku a kan abu ya cuce ku. Ba zan tilasta ku ku yi wani abu ba, amma shawarata ita ce, ku yi hankali, ku karanta takarda, ku fahimce ta kafin ku sa mata hannu. Har da kai Zakari.

**MAI GABATARWA**:

John ya ɗauki shawarar Metogba, kuma ya ƙi yarda ya sa hannu a kan kwanturagin a yanzu. Ba da jimawa ba, sai motar Honourable Gambo ta ja birki a gaban gidan Anti Lily.

**Fitowa ta 4: A gidan Anti Lily**

Honourable Gambo, Anti Lily

**ANTI LILY:** Na gode ƙwarai da gaske, da kuma taimaka min da ka yi a filin wasa.

**HON. GAMBO:** Ba kome. Wato har yanzu ba kya so ki gaya min gaskiyar abin da ya faru da cikin da kika yi? Kin zubar da cikin ne, Lily? Na ce ki yi haƙuri saboda na gudu na bar ki. Ina so in san gaskiyar abin da ya faru ne kawai, daga nan sai in ƙyale ki, Lily.

**ANTI LILY:** Wai kai har yanzu idanuwanka a kulle suke ne? Zan faɗa maka. Ban zubar da cikin ba. Na haifi yaro namiji, na sa mishi suna, kuma na gudu na bar shi kamar yadda ka yi. Mummunar shawarar da na taɓa ɗauka a rayuwata.

**HON. GAMBO:** Don Allah, faɗa min sunanshi mana? Ni kuwa zan nemo shi. Wane suna kika sa mishi don Allah?

**ANTI LILY:** Ba sai ka nemo shi ba. Ka san shi. Yanzu ka gama kallonshi ya ci ƙwallo a wasan da aka yi.

**MAI GABATARWA:**

Mamaki, rashin gaskiya da ruɗewa sun buge Honourable Gambo a lokaci guda. Yanzu ya yi ido-da-ido da abin da ya shuka a da a rayuwarshi bayan ya ɓace na lokaci mai tsawo kamar ba za a ƙara ganinshi ba. Sannan 'yan

makwanni a gaba, ranar da yara 'yan wasa za su fita zuwa ƙasashen Turai ta zo. Kuma duk sun taru a filin jirgin sama, zagaye da 'yan jaridu, 'yan'uwa, abokai da masu fatan alheri.

**Fitowa ta 5: A filin jirgin sama**

Zakari, Safina, John, Honourable Gambo, Anti Lily

**JOHN:** Zaks, na ji daɗi da ban sa hannu a kwanturagin nan ba. Da sai in riƙa aiki a gidan sai da abinci kwanaki biyar a mako, sannan in riƙa buga ƙwallo a ranaku biyu kawai! Kuma duk ba tare da ana biyana ko kwabo ba!

**ZAKARI:** Haka ne, amma kar ka damu. Na tabbata cewa za ka ɗauki hankalin wasu ƙungiyoyin a yayin da muka je Turai. Yauwa, ga Safina nan tare da antinta.

**SAFINA:** An gai da ƙwararren 'yan wasa. John, yaya gari? Sannunku dai!

**JOHN:** Yauwa, a gai da Safina! Ya yi kyau da kuka zo nan. Jama'a lokaci ya yi da za mu shiga jirgi. *Bye Dad!*

**HON. GAMBO:** To ɗana, Allah ya kiyaye! Kuma Allah ya ba da sa'a!

**SAFINA:** Anti Lily, sai mun dawo! Ki gai da min da iyayena.

**ANTI LILY:** To shi ke nan, Safina. Allah kai ku lafiya! Ki kula da kanki, 'yata.

**ZAKARI:** To shi ke nan, jama'a, sai wani lokacin.

**ANTI LILY da HON. GAMBO:** Sai wani lokaci, ɗanmu!

**MAI GABATARWA:**

Jim kaɗan bayan jirgin ya tashi zuwa sararin samaniya, Zakari ya kasa daurewa, sai da ya zubar da hawaye saboda maganar da ya ji ta ƙarshe. Sai kuma wani tunani na mamaki ya faɗo mai zuciya. Wai ko gaskiya ne cewa, Honourable Gambo da Anti Lily, su ne iyayenshi na gaskiya? Ko kuwa dai suna so su yi amfani da sunan da suka ga yana yi ne yanzu? Amma wannan, wata magana ce ta wani lokaci, saboda a yanzu mun kawo ƙarshen wannan wasa a kan harkar wasan ƙwallon ƙafa a Afirka. Kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe, domin jin duka waɗannan shirye-shirye da kuma wasu.

---

**'Yan wasa:**

Ibrahim Ishaq Ɗan Uwa Rano
Sadiq Murtala Mansur
Rabi Salman
Awal Yahya Abdu
Mustapha Sidi (Chuba)
Abdullahi Sani Shu'aibu
Hadiza Jinta
Lawal Gwazaye
Abdullahi Garba
Yusuf Idris
Aminu Auwalu